Alkiyama ba za ta tsaya ba har sai mutum ya wuce wani kabari sai ya ce: Ina ma dai ni ne a wurin nan

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - daga Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Alkiyama ba za ta tsaya ba har sai mutum ya wuce wani kabari sai ya ce: Ina ma dai ni ne a wurin nan".
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agar shi - ya bada labarin cewa Alkiyama ba za ta tsaya ba har sai mutum ya wuce kabari, sai ya yi burin ya zama matacce a bigirensa, sababi shi ne tsoronsa akan kansa na tafiyar Addininsa saboda rinjayar karya da ma'abotanta, da bayyanar fitintinu da sabo da abubuwan ki.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/65022